# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Shekaru Arba'in



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**



**Sa’ad da Allah ya kubutar da Isra’ilawa daga Masar, Musa ya jagorance mutanen a cikin sujada.  Ya yi wakar yabo.  “Zan yi waka ga UBANGIJI gama ya ci nasara cikin daukaka.”  Musa ya yi waka game da dukan manya abubuwan da Allah ya yi wa Isra’ila.**



Bayan kwana uku a hamada mutanen masu kishin ruwa suka samu dan wurin ruwa. Amma ba su iya shan ruwa mai daci ba. Maimako su yi addu'a, mutanen suka fara gunaguni. Allah yana da kirki.



Sai ya mai da ruwan ya zama mai kyau domin a sha.



**Ya zama cewa mutanen sun yi gunaguni a kan kome. “Mun kasance da abinci a Masar. A hamada za mu mutu da yunwa.” Suka yi kuka. Da yamma a ranar nan Ubangiji ya aika da tsuntsaye kamar kananan makarwa. Mutane suka kakkama su da sauki.**

Washegari Allah ya aika da manna. Manna wani iri burodi ne wanda zakinsa kamar biskit mai zuma.

Kowane safe manna yana kwanciya a kasa a shirye domin a kwashe.



Ta haka ne Allah ya ciyar da mutanen sa a hamada.

**Kowace rana sun sa rai ga Allah domin sabon abinci. Amma wadansu mutane suka tattara fiye da suke bukata, ko da yake Allah ya ce zai ruba idan ya kwana har safe.**



**Babu shakka, manna na jiya yana cike da tsutsa – amma ban da na ranar hutun Asabar. A rana ta bakwai na musamman mutanen sukan huta sai su ci na jiya.**



Allah ya lura da Isra’ilawa a hamada. Ya ba su abinci da ruwa – ya kuma tsare su daga abokan gaba. Sa’ad da Amalekawa suka kawo hari,

Isra’ila ta yi ta cin nasara a yake-yaken muddin Musa yana rike da sandan Allah.





**Allah ya ce wa Isra’ilawan, “Idan kun yi biyayya ga Muryana za ku zama mutanena na musamman.” “Duka abin da Allah ya ce za mu yi,” mutanen suka gaya wa Musa. Sai suka kai gindin Tudun Sinai suka jira Musa yayinda Musa ya tafi domin ya sadu da Allah.**



Musa ya kasance da Allah a Tudun har kwana arba’in. Allah ya rubuta Dokoki Goma a kan alunan dutse. Ya gaya wa Musa yadda yake so mutanensa su yi rayuwa.

**1. “Ba za ku kasance da wadansu alloli a gabana ba.”**

**2. “Kada ku gina ko ku bauta wa wani siffa.”**

**3. “Kada ku kira sunan UBANGIJI a banza.”**

**4. “Ku tuna da ranar Asabar, ku kiyaye shi da tsarki.”**

**5. “Ku girmama ubanku da uwarku.”**

6. “Ba za ku yi kisa ba.”

7. “Ba za ku yi zina ba.”

8. “Ba za ku yi sata ba.”

9. “Ba za ku yi karya ba.”

10. “Ba za ku yi kwace.”



**Lokacin da Musa yana tara da Allah a Tudun Sinai, Isra'ilawa suka yi wani abin ban tsoro. Suka umarci Haruna ya gyara musu wani gunkin shanu – sai suka yi masa sujada maimakon Allah. Allah ya yi fushi. Haka ma Musa.**



**Sa’ad da Musa ya ga Gunkin Zinariyar da yadda mutane suke rawa kewaye da gunkin, ya tattake allunan duwatsun a kasa.  A cikin fushi Musa ya lallatar da gunkin zinariyan. Mugayen mutanen da suka yi wa gunkin Sujada an karkashe su.**

Allah ya sake yin wadansu
allunan duwatsu guda biyu.
Ya gaya wa Musa ya gina
Tabanakul – wani babban tenti
mai katanga kewaye da shi – inda
Allah zai kasance tare da mutanensa.
Za su yi sujada ga Allah a wurin.
Tulin hadari da wuta a sama suka
nuna cewa Allah yanan
nan a wurin
tare da su.



**Sa’ad da suka yi kusa da Kan’ana, sai Musa ya aike ‘yan leken asiri guda goma sha biyu domin su ga kasar da Allah ya yi wa mutanensa alkawari. ‘Yan leken asirin dukansu suka yarda cewa kasar tana da kyau! Amma guda biyu ne kawai, Yoshuwa da Kaleb, sun ba da gaskiya cewa za a ci nasara a kan kasar tare da taimakon Allah.**



**Guda goma sun ji tsoron birane masu karfi a wurin da dogayen mutanen da suka gani a kasar. “Ba za mu iya kwace kasar ba,” suka yi kuka. Sun manta da manyan abubuwan da Allah ya riga**

**ya yi domin ya ‘yantar da su daga Masar.**



**Mutanen sun bi ‘yan leken asiri guda goma. Suka yi kuka suka shirya su koma zuwa Masar. Har suka yi kokari su kashe Musa. Allah ya cece ran Musa. Sai ya gaya wa Mutanen, “Shekaru arba’in za ku yi ta yawo a hamada. Kaleb da Yoshuwa da ‘ya’yanku ne kadai za su rayu su shiga kasar da kun ki.”**



# Shekaru Arba'in

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Fitowa 15 zuwa Kidaya 14

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

12

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**